







Zomo da Kurege abokan juna ne.

Suna zaune a garin Manki.

Manki garin manoma ne.

Kurege ba ya son aiki.

Kullum yana bacci






Zomo ba shi da lalaci.


Zomo yana yin noma.

Yana noma abincinsa.

Damina ta zo.

Zomo ya share gonarsa.





Zomo yayi aiki a gona.

Ya shuka gero.



Ya shuka dawa.

Ya shuka gyaɗa da wake.

Kurege bai gyara gona ba.


Yana bacci a gida.



Lokacin girbi ya zo.

Zomo ya sami amfani da yawa.



Zomo ya ci ya koshi.

Yanzu ne lokacin bacci.